| | |
|---|---|
| **JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA** | **7 Ramadhan, 1443** |
| **MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI** | **8 Afrilu, 2022** |

# IMANI DA KYAWAWAN ƊABI'U A CIKIN AZUMI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Ku yi gaggawa wajen aikata ayyuka na gari; domin ku sami babban gafara daga Allah da yake mallakar al'amurran ku, ku kuma sami shiga aljannar da faɗin ta ya kai faɗin sama da ƙasa, an tattale ta ne saboda masu tsoron Allah da masu nesantar azabar sa. Su kuwa waɗanda suke ciyar da dukiyoyin su a lokacin da suke cikin yalwa da ƙunci; da lokacin da suke da iko, ko suke da rauni; domin neman yardar Allah, suke kuma hana zukatan su azabtar da wanda ya munana masu, suke kuma yafiya ga waɗanda suka yi masu laifi, lallai waɗannan suna cikin mutanen kirki masu kyautatawa; kuma lallai Allah Maɗaukakin Sarki yana bai wa mutanen kirki da masu kyautatawa lada, yana kuma yarda da su)** [Ali Imran: 133 – 134], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai Allah mai girma da buwaya ya wajabta yin azumi ne, saboda wasu manyan manufofi, da hikimomi masu girma, azumi makaranta ne na imani, da ƙarin kyautata ɗabi'u, duk wanda yake yi wa Alƙur'ani mai girma kallo na lura, zai ga inda Allah

mai girma da ɗaukaka ya ambaci babban manufar da azumi yake tabbatarwa, Allah mai girma yana cewa: **(Ya ku waɗanda kuka yi imani, Allah mai girma ya shar'anta wajibcin Azumi domin tsarkake zukatanku da daidaita sha'awarku, da fifita ku akan dabbobin da suke bin sha'awarsu, shi wannan wajabta Azumi da aka yi maku kamar yadda aka farlanta wa al'ummomin da suka gabace ku, ba zai yi maku wahala ba, saboda wajibi ne akan mutane baki ɗaya, wajibcin Azumi da tsayawa dominsa duka domin rainon ruhin tsoron Allah a cikinku ne, da kuma ƙarfafa zukatanku da tsarkake su)** [al- Baƙra: 183], tsoron Allah wani hali ne da ya game dukan ɗabi'un alhairi; saboda haka ne ma ya zo a gwame da ɗabi'un imani, da kyautata hali masu yawa a cikin Alƙur'ani mai girma, Allah mai girma yana cewa: **(Kai, lallai mutane sun yawaita magana akan al'amarin alƙibla, kai kã ce ita ce alhairi ita ɗaya kacal, wannan kuma ba shi ne gaskiya ba, ba fuskantar wani sashe a gabãshi ko yammaci shi ne kashin-bayan addini ko matattara alhairi ba, matattara alhairi yana cikin abubuwa ne masu dama, wasu suna cikin rukunnan ingantacciyyar aƙida ne, wasu kuma suna cikin tushen ayyuka na gari da ibadu. Na farko shi ne: imani da Allah, da ranar tashin alƙiyama, da hisabi, da abubuwan da za su biyo bayan haka a ranar alƙiyama, da imani da mala'iku da littattafan da aka saukar wa Annabawa, da ma su kansu Annabawan. Na biyu shi ne: bayar da dukiya cikin jin daɗin rai ga talakawa, makusanta da marayu da waɗanda buƙatu da rashi suka yi masu yawa, da matafiyan da guzuri ya yanke masu, ba su da abin da zai isar da su zuwa ga manufarsu, da masu roƙon mutane da buƙata ta tilasta masu yin haka, da kuma ciyarwa don manufar 'yanta bayi da 'yanta wuyayensu ga barin bauta.**

**Na uku: kiyaye sallah. Na huɗu: fitar da zakkar da aka wajabta. Na biyar: cika alƙawari a rai da dukiya. Na shida: haƙuri akan cutar da za ta faɗa wa rai ko dukiya, ko lokacin haɗuwa da abokan gaba a wurin yaƙi. Waɗanda suka haɗa waɗannan aƙidu da ayyuka na alhairi su ne waɗanda suka yi gaskiya cikin imaninsu, su ne waɗanda suka ji tsoron kafirci da ƙasƙanci, suka kuma nesance su)** [al- Baƙra: 177].

A cikin sassa, da ɓangarorin imani, da kyautata ɗabi'u a cikin azumi, akwai ɗabi'ar hararo Allah a cikin komai, a kuma dukan yanayi, lallai azumi sirri ne da yake tsakanin bawa da Ubangijinsa, babu wanda yake iya saninsa sai Allah, wannan babban dalili ne da yake nuna yaƙinin da bawa yake da shi na cewa lallai Allah yana ganinsa a lokacin da yake a ɓoye, da lokacin da yake a fili, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ya Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), lallai ka isar da saƙo, Allah ya san haka, ba ka taɓa kasancewa a cikin wani al'amari cikin al'amurranka, haka ma ba ka taɓa karanta Alƙur'ani, ka yi aiki da shi, kai ko al'ummarka ba face mun yi maku shaida muna ganin lokacin da kuke shiga cikin domin yin jahadi, babu wani abu daidai da ƙwayar zarra a ƙasa, ko a sama da yake iya ɓuya wa Ubangijinka, kai babu abin da yake ƙasa da haka, ko yake sama da haka da yake iya ɓuya. Lallai duka waɗannan abubuwan suna nan a rubuce a wurin Allah dalla- dalla)** [Yunus: 61], saboda wannan ma'ana ta muraƙaba ce ya zama babu wanda ya san girman ladan da mai azumi yake samu banda Allah mai girma da ɗaukaka, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Dukan ayyukan ɗan Adam ana ruɓanya masa lada, aiki mai kyau guda ɗaya ana ruɓanya masa kwatankwacinsa sau goma, zuwa har**

**ninki ɗari bakwai, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: banda azumi, wannan kam nawa ne, ni ne kuma zan bayar da sakayya akansa, ya bar sha'awarsa, da abincinsa saboda ni)**, lallai ya kamata mai azumin yake hararo Allah a cikin azuminsa ya hararo shi mai girma da ɗaukaka a cikin ayyukansa, da sana'arsa, da sauran dukan mu'amalolin da yake yi a watan Ramadhan, da ma sauran watanni.

Azumi makaranta ne na koyon dukan nau'o'in haƙuri; a cikin azumi akwai haƙuri da juriya wajen gabatar da biyayya ga Allah, da kuma haƙurin kamewa, da nesantar abubuwan da aka haramta, da haƙurin kamewa sha'awa; saboda haka ne Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya sifanta watan Ramadhan da cewa wata ne na haƙuri, Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Azumin watan haƙuri, tare da kwanaki uku na kowane wata, daidai yake da azumtar dukan shekara),** lallai ya kamata mai azumi ya zama yana da haƙuri, ya danne fushinsa, ya kuma yafe wa wanda ya zalunce shi, ya bai wa wanda ya hana shi, ya kyautata wa wanda ya munana masa, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(A duk ranar da wani daga cikinku yake azumi, to kada ya yi maganganun batsa, kada kuma ya faɗa- faɗa, idan wani ya zage shi, ko ya neme shi da faɗa, to ya ce masa: ina azumi).**

Haka ma mai azumi na gaskiya ba ya ƙarya, ba ya algushi, ba ya yaudara, ba ya ha'inci, ba kuma ya yi da wani, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk bai bar maganar ƙarya, da aiki da ita ba, to lallai Allah ba ya buƙatar ya bar abincinsa, da abin shansa)**.

****

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai a cikin manyan manufofin azumi akwai taimako, da tausayi, da jin halin da talakawa da mabuƙatan da suke kusa da shi suke ciki, hakan ya kai shi ga tausaya masu, da sauƙaƙe masu damuwa, da biya masu buƙata, lallai an tambayi Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) cewa: Wane aiki ne a Musulunci ya fi zama alhairi? Sai (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Ka ciyar da binci, ka kuma yi sallama ga wanda ka sani da wanda ba ka sani ba).**

Idan har ladan jin tausayi, da bayar da taimako, da baiwa, da ciyar da abinci yana da girma a dukan lokuta, to lallai girmansa ya fi bayyana a watan Ramadhan, falalarsa ya wuce na sauran lokuta, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya shirya wa mai azumi kayan buɗa baki, yana da lada kwatankwacin na mai Azumin, ba kuma tare da an rage ladan mai azumi da komai ba)**, Sayyiduna Abdullahi Bn Abbas (Allah ya ƙara yarda da su) yana cewa: **Lallai Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya fi dukan mutane bayar da kyauta da baiwa da alhairi, a watan Ramadhan kuwa abin babu magana.**

Lallai abu ne mai matuƙar kyau a ce mun koyi darussan imani, da na kyawawan ɗabi'u a wannan makaranta ta Azumi, ta yanda hakan zai ba mu daman isa zuwa ga babban manufar azumin ta haƙiƙa, Sayyiduna Jabir Bn Abdullahi (Allah ya ƙara yarda da su) yana cewa: **Idan har ka yi azumi, to kunnenka, da idanuwanka su ma su yi azumi, harshenka ya kame ga barin**

ƙarya da saɓon Allah, ka nesanci cutar da maƙwabci, ka zama cikin hankali da natsuwa a tsawon yinin azuminka.

Ya Allah Ubangiji ka kare mana ƙasarmu, da sauran ƙasashen duniya baki ɗaya.